

# HAƊUWA DA AL'UMMA TAIMAKO

## Bayanai ga Iyaye Game da Hukumar Lura da Ayyukan Tallafi ga Masu Naƙasun Fahimta da Girma (LIDDA)

Ku samu wannan a kan intanet

Idan an ayyana yaranku a matsayin masu fuskantar **nakasu a fannin fahimta ko tsaiko a fannin girma**, ɗaya daga cikin matakai na farko masu muhimmanci shi ne tuntubar LIDDA. Shafukan da aka kawo a kasa suna ɗauke da bayanan da kuke bukata domin samowa tare da tuntubar LIDDA a ƙasarku.

Bayanai game da nau'ukan nakasa domin cancantar karatu na musamman

### Mene ne LIDDA?

LIDDA sun kasance matakai da ake bi domin shiga cikin tsarin tallafin al'umma na Masu Nakasa a Fannin Fahimta da Cigaba (IDD) a Texas. Kowace hukumar LIDDA tana aiki a wani yanki na musamman sanan ita ce take da alhakin taimaka wa iyalai domin su samu tallafi na tsawon lokaci wanda zai ba wa yara da matasa damar rayuwa da samun ɗaukaka a cikin al'ummar da suke.

### Bayanan Tuntuɓar Makaranta:

Ku tuntubi wanda ake tuntuba a makarantar ɗiyanku idan kuna da wasu tambayoyi game da samun LIDDA ɗinku ko idan kuna bukatar taimako domin samun damar shaga kafafen intanet da suke da alaka da wannan takardar.

| | |
|---|---|
| **Suna:** | |
| **Matsayi:** | |
| **Imel:** | |
| **Lambar Waya:** | |

### Bayanai game da nau'ukan nakasa domin cancantar karatu na musamman:

- **Tuntuɓa da shiga cikin tsarin:** Samar da bayanai game da ayyuka da taimako, tantancewa idan yaranku sun cancanci cin moriyar IDD, da kuma taimaka wa iyalai wajen tura bukatar samun karin kuɗin riƙe kai (SSI), inshoran masu nakasa (SSDI), da kuma Medicaid
- **Ka'idojin shirin:** Taimaka wa iyalai wajen samun tallafi da suka shafi kiwon lafiya da karatu da walwala
- **Ɗauke nauyin reno na wani lokaci:** Ɗauke nauyi na wani lokaci a lokacin da asalin mai reno ba sa nan
- **Keɓantattun tallafi ta la'akari da bukatu da wadata:** Samar da tallafi kamar taimako ta fuskar samun aiki, reno, shawarwarin rayuwa, da kuma nau'ukan tallafi na musamman. Yana da kyau a lura da cewa waɗannan ayyuka suna iya bambanta daga yanki zuwa yanki.
- **Shirye-shiryen Medicaid:** Sanya sunayen mutane a cikin jerin sunayen waɗanda za a ɗaga wa ƙafa a karkashin shirin Medicaid tare da taimaka wa waɗanda suka cancanci shiga cikin shirshe-shiryen Medicaid

SPEDTEX Special Education Information Center · TEA Texas Education Agency · Texas SPED Support



# HAƊUWA DA AL'UMMA TAIMAKO

## Bayanai ga Iyaye Game da Hukumar Lura da Ayyukan Tallafi ga Masu Nakasun Fahimta da Girma (LIDDA)

### Shirye-Shiryen Tallafi na Medicaid

Texas tana gudanar da shirye-shiryen tallafi na Medicaid masu yawa waɗanda suke samar da ayyuka da taimako na tsawon lokaci ga waɗanda suke da nakasa a cikin al'ummarsu. Kowane shiri yana gabatar da aiki na daban sannan yana da **jerin masu so** nasa. Wakilin LIDDA na yankinku zai iya taimaka muku wajen fahimtar zaɓin da zai fi dacewa da ku ta la'akari da baiwar ɗiyanku a yanzu da kuma nan gaba tare da tallafin da ake bukata.

- Shirye-Shiryen Tallafi da Taimaka wa Al'umma (CLASS) — dukkannin shekaru
- Kurame da Makafi Masu Nau'ukan Nakasa Daban-Daban (DBMD) — dukkannin shekaru
- Shirye-Shiryen da Suka Shafi Gida da Yanki (HCS) — dukkannin shekaru
- Shirin Yara Masu Lalurar Rashin Lafiya (MDCP) — 'yan shekara 20 ko ƙasa da haka
- STAR+PLUS Home and Community Based Services (HCBS) — yan shekara 21 zuwa sama
- Texas Home Living (TxHml) — dukkannin shekaru
- Shirye-Shiryen Karfafa Matasa (YES) — shekaru 3 zuwa 18

### Mene ne ma'anar "Jerin Masu So"?

A wasu lokutan akan kira jerin masu so da suna "jerin masu jira." Ana sanya mutane a cikin wannan jeri bisa tsarin wanda ya fara zuwa. Idan sunan mutum ya kasance a saman jerin sunayen, to za a tuntuɓi mutumin daga Hukumar Lafiya da Walwalar Jama'a (Health and Human Services Commission) (HHSC) ko kuma wani wakilin LIDDA. Samun damar shiga cikin shirin ya danganta da kuɗin da ake da shi, sannan mutane suna iya kasancewa a cikin jerin masu so na tsawon shekaru kafin a tuntuɓe su.

#### Muhimman Bayanai:

- **Ku sanya sunan ɗiyanku a cikin jerin sunayen masu so na shirye-shiryen tallafi na Medicaid da zarar an fuskanci suna da wata nakasa** (a duba shafi na 3). A koyaushe kuna iya daina karɓar taimako idan bukatar hakan ta kau a nan gaba.
- Ba kwa bukatar nuna cewa kun cancanta kafin a sanya ku a cikin jerin masu so.
- Ku tabbatar da cewa bayanan tuntuɓarku suna aiki domin a samu damar tuntuɓar ku.
- Ku riƙa bincika matsayin ɗiyanku a kowace shekara. Bincikawa a daidai lokacin zagayowar ranar haihuwar ɗiyanku yana da matukar muhimmanci domin zai taimaka muku wajen tuna yin hakan.

SPEDTEX Special Education Information Center

TEA Texas Education Agency

Texas SPED Support



# HAƊUWA DA AL'UMMA TAIMAKO

## Bayanai ga Iyaye Game da Hukumar Lura da Ayyukan Tallafi ga Masu Nakasun Fahimta da Girma (LIDDA)

## Haɗu da LIDDA a Yankinku:

- **Ku tambayi kwamitin ɗaukar ɗalibai da dubawa da kora (ARD) na makarantar ɗiyanku** game da wurin da za ku samu bayanai game da LIDDA da take aiki a kasarku.
- Tuntuɓi LIDDA din ku don **tsara taron farko.**
- Yayin zaman tattaunawa, ma'aikacin LIDDA zai tattauna da ku game da **zaɓukan da ake da su dangane da ayyuka da jerin masu so** da ya dace da bukatun ɗiyanku.

## Tambayoyin da za ku yi wa Jami'in Hulɗa da Jama'a na LIDDA ɗinku:

- Waɗanne ayyuka ne ake gudanarwa ta hanyar LIDDA?
- Ta yaya zan sanya sunan ɗiyana a cikin jerin masu so na shirye-shiryen tallafi na Medicaid?
- Waɗanne takardu ne ake bukata in gabatar?
- Da wa zan iya magana idan ina da karin tambayoyi game da ayyuka da taimako da za a iya ba wa ɗiyana?
- Shin akwai wasu karin hukumomi da shirye-shirye da ake da su domin ɗiyana?

## LIDDA ta Kasata:

**LIDDA Nawa:**

**Imel:**

**Lambar Waya:**

**Kafar Intanet:**

Ku ziyarci [Kafar intanet ta HHSC domin duba LIDDAs] ta amfani da kasa ko lambar yanki.

## Karin Bayanai:

- Texas HHSC:
  - Bayanan LIDDA
  - Rage Jerin Masu So
- YourTexasBenefits.com
- The Arc of Texas
- Navigate Life Texas: Tallafi da Jerin Masu Su
- Hukumar Karatu ta Texas (Texas Education Agency) (TEA)
  - SPEDTex
  - Matakan Samun Bayanan Samar Da Sauye-Sauye a Texas (Roadmap to Texas Transition Resources)
  - Bayanai da taimako da ake da su: Ku kasance cikin jerin masu so yau (Jerin Bidiyoyin Magana Kai Tsaye): Ingilishi | Sifaniyanci | Vietnamese

SPEDTEX Special Education Information Center | TEA Texas Education Agency | Texas SPED Support